*International Journal of Innovative Language, Literature & Art Studies 13(1):25-36, Jan.-Mar., 2025*

© SEAHI PUBLICATIONS, 2025 www.seahipublications.org ISSN: 2467-8511

doi:10.5281/zenodo.14805150

# Jerin Sunaye Da Tarihin Wasu Maroqan Baka Na Hausa Na Jihar Katsina

**Ibrahim Bala Maidabino**

**Department Of Primary Education**
**Isa Kaita College Of Education, Dutsin-Ma, Katsina State, Nigeria**
**(08161306979 08025993647 namaidabino@yahoo.co.uk)**

**Tsakure**
Maroqa na xaya daga cikin rukunin masu sana'ar adabi a qasar Hausa, waxanda da ba su samu kulawar masu nazari sosai kamar takwarorinsu mawaqa da marubuta ba. Haka kuma ga alama, karsashin sana'ar na dusashewa. Wannan bincike da aka aiwatarwa ta hanyar hira da masu ruwa da tsaki a harkar adabin baka a jihar Katsina tare da naxa da kuma nazarin ayyukansu ya shafi masu yin roqon baka a matsayin sana'a. Wato mutanen da ke yin sana'ar roqo a wuraren bukukuwa ko duk inda suka samu taron jama'a da kuma masu yi tare da mawaqa ko makaxa. Wannan bincike bai tavo komai game da masu maula da mabarata da almajirai waxanda ba maroqa ba. Dalili kuwa a nan shi ne, jama'a ba su xauke su a matsayin qwararrun masu ayyukan adabi ba. Kuma ba a xauki yin su a matsayin karvavviyar sana'a ba a qasar Hausa. Muhimmancin wannan muqala ya haxa da qarin haske a kan makomar wannan daxaxxiyar sana'a a qasar Hausa.
**Muhimman Kalmomi:** Roqo, Hausa, Katsina, Adabi, Bambaxanci.

## Gabatarwa

Sana'ar roqo na xaya daga cikin manya, kuma daxaxxun sana'o'i a qasar Hausa. Wani abin mamaki shi ne, wannan sana'a ta roqo ba ta samu gamsassar kulawa ga masu nazari ba. Kula da yawan maroqa a cikin qasar Hausa da kuma muhimmiyar rawar da suke takawa wajen nishaxantarwa da kuma qara wa gwarazansu qwarin gwiwa wajen aikata wani abin kirki a cikin al'umma, ya sa ganin dacewar masana da manazarta da xalibai masu bincike su mayar da hankali wajen taskace yadda wannan sana'a take a qasar Hausa. An yi ayyuka na a-zo-a-gani dangane da waqoqin Hausawa da sauran wasu vangarori na adabi Hausawa, amma an bar wani wagegen givi dangane da abokan tafiyarsu, wato maroqa.

Wannan aiki ya kevanta ga maroqan jihar Katsina kaxai ne. Domin samun qalailaice bayanan su maroqan, dangane da dalilansu na xaukar sana'ar roqo (gado suka yi ko haye). Haka kuma a cikin binciken an tattaro wasu matanonin roqon da wasu maroqa suka yi wa iyayen gidajensu. Haka kuma akwai tsokaci dangane da muhimmancin sana'ar roqo a qasar Hausa. Wannan muqala ta kuma waiwaiyi tarihin wasu xaixaikun maroqa na wurare daban-daban na cikin wannan jiha.

## Matsalar da Kuma Hujjar da ta Haifar da Bincike

Da yawa daga cikin mawaqa da maroqan baka har ma da marubuta na rasuwa, kuma tarihinsu na shuxewa. Haka kuma ana samun sauyi wajen aiwatar da waqoqin baka na Hausa da qarin farraqarsu da maroqan baka ya haddasar da matsalar da ta haifar da wannan bincike. Ganin ba wani aiki kamar littafi ko maqala wadda aka buga da ya qunshi tarihi ko sunayen maroqan qasar Hausa (kamar yadda yake ga mawaqan baka na Hausa) ya sa tunanin cewa ya wajaba a yi wani aiki da za ya taskace wani abu dangane da sana'ar roqo.

**Manufofin Bincike**

Wannan bincike ya qudurci zaqulo tare da tattaro sunaye da tarihin wasu masu sana'ar roqon baka na cikin Jihar Katsina da taskace wasu ayyukan (matanoninn) wasu maroqan baka na jihar Katsina da Gano makomar sana'ar roqo a jihar Katsina da kuma matsalolin da sana'ar roqo ke fuskanta tare kuma da gano maganinsu.

**Amfanin Bincike**

Binciken zai amfanar wajen yin nazarin Adabin Hausa a manyan makarantun gaba da sakandare na Arewacin Nijeriya a sassan nazarin Hausa. Amfanin binciken zai kai ga malamai masu koyarwa (a matsayin littafin tuntuva) da kuma ga xalibai masu neman ilimi. A vangaren gwamnati kuma, binciken zai amfanar wajen ba ta haske a lokacin yanke wani hukunci game da masu ayyukan adabi ko kan samar da ayyukan yi ga jama'a.

Kodayake, aikin ya kevanta ga masu ayyukan adabin a cikin jihar Katsina, aikin za ya bayar da haske mai muhimmanci wajen gane qiyasin yawan maroqa a qasar Hausa.

**Roqo (ma'ana da tarihi)**

Roqo a Magana ta yau da kullum na nuni da neman wani ya bai wa wani ko ya aikata wani abu ga wani. A cikin wannan aiki ma`anar ba ta sauya ba sai dai hankali ya karkata g asana`ar roqon baka wadda akan yi amfani da basirar Magana wajen gwarzanta wani ko ta bayyana asalinsa da ayyukansa ko na magabatansa masu qara masa qima domin y aba su abin hannunsa. Masu irin wannan sun xauki yin roqo a matsayin sana`a. bayan haka, kuma kodayake sun san abin da aka bas u ko yi masu a matsayin sakamakon roqon da suka yi, suna kuma kallon abin a matsayin ladar aikin da suka yi na roqo.

**Muhimmancin Roqo**

Roqo ga masu yin shi na a matsayin sana'a. Hakan na nuna cewa roqo na zaman hanyar neman abin rufin asiri ga wasu jama'a a qasar Hausa. Bayan wannan muhimmanci na roqo, akwai wasu fa'idoji da yawa da sana'ar roqo take da su a qasar Hausa.

1. **Hanyar samun kuxin shiga ga maroqa.**
   Kamar yadda bayani ya gabata a sama, roqo na a matsayin sana'a ga masu yin shi. Hakan ya tabbatar mana da matsayin roqo na zama hanyar samun kuxin shiga ga maroqa. Maroqa na samun kuxi da sutura da ababuwan hawa da kayan abinci daga waxanda suka wasa ko yi wa kirari. Wato waxanda aka roqa.
2. **Inganta wasu ayyukan adabi da al'ada**
   Sana'ar roqo na qara inganta ko qara armashi a yayin da ake aiwatar da wasu ayyukan adabi, musamman waqar baka. Tsoho (2010) ya kawo muhimmancin maroqa da yawa a wajen aiwatar da waqoqin baka na Hausa.
3. **Hanyar sadarwa ga Hausawa**
   Maroqa kan kasance masu sanar da wasu muhimman abubuwa ga jama'a. Alal misali, maroqa ne ke yin shela a cikin gari domin isar da saqon hukuma ga jama'ar gari a qasar Hausa. Haka kuma a wajen bukukuwan xaurin aure da raxin suna, maroqa ne ke isar da saqon limamai wajen mahalarta. A wurare da yawa, musamman a karkara, maroqa ke sanar da lokuttan aiwatar da wani taro ta hanyar fara halartar wajen da kuma yin gangamin a fito lokaci ya yi (hira da Tunkiya a ranar 2024).
4. **Samar da nishaxi ga Hausawa**
   Haka kuma maroqa na qara armashin taro ta sanya raha da nishaxi wajen duk wani taron da al'umma suka haxu. Maroqa gwanaye ne wajen yin abubuwan ban dariya. Gaskiya wasu mutane na ganin duk taron da ba maroqa a ciki, tamkar miyar da ba gishiri ce (hira da sanqiran maraxin Katsina Hakimin Kurfi a 2024)
5. **Adana tarihi**
   Maroqa mutane ne ne da kan bi diddqin tarihin qwarzonsu domin faxar salsalarsa da nasabarsa ga jama'a yadda za ya qara kwarjini da xaukaka. Wasu mutane bas a sanin cikakkakiyar nasabar abokan zamansu sai ta hanyar maroqa a yayin da suke aiwatar da sana'arsu ga a wajen buki. Haka kuma maroqa na faxar tarihin faruwar wani abu muhimmi da ya afku (misali tafiye-tafiye

ko gagarumin bukin karramawa da sauransu) ga wanda suke wa kirari ko wani makusancinsa (hira da Haro Mati na Qauyen Andu a qauyen Laya ranar 3/3/2024).

6. **Tunzurawa**
   Tunzurawa ita ce harzuqa ko sanya wani ya aikata wani abu wanda bai nufaci aikayawa ba (Said, 2007). Halin maroqa ne tunzura gwarazonsu a cikin kirari. Sukan kambama shi yadda za ya gane matuqar girma da darajarsa a cikin al'umma. Hakan na sa ya ji cewa shi babba ne kuma mai daraja da xaukaka. Don haka sai ya cire duk wani tsoro da fargaba ya kuma aikata ko ya yi alwashin aikata duk wani abun da aka nemi ya aikata don ya tabbatar da matsayin da aka xora shi a kai.
7. **Tarbiyantarwa**
   Maroqa kan ambaci wani kyakkyawan hali na magabacin wanda suke yi wa roqo tare da danganta wanda ake wa roqon da waxannan halaye. Hakan kan sanya wanda ake roqon ya kyautata halayensa ta kwatanta tafiyar da rayuwarsa kamar yadda magabacinsa ya yi. Ta haka ne sana`ar roqo ke qara tarbiyantar da Hausawa.

**Wurida Lokacin da ake Aiwatar da Roqo**

Komai da muhallin aiwatar da shi. Shi ma roqo yana da lokaci da bagiran da suka yi fice wajen yin sa. Hausawa na aiwatar da sana'ar roqon baka a duk in da wani abu ya tara jama'a, in dai ba taron jana'iza ba ne (Hira da Haro Musa ranar 3/3/2024). Misalan irin tarurrukan da maroqa ke baje-kolinsu, sun haxa da wuri da lokacin aiwatar da taron suna da na xaurin aure da na hawan salla da na siyasa da naxin sarauta da sauransu.

Maroqa na aiwatar da sana'arsu a lokacin da ake aiwatar da waqar baka ko kixe-kixe. Wani fitaccen lokacin aiwatar da roqo kuma shi ne lokacin yi wa yara kaciya (Hira da Tunkiya Ingawa) da lokutan aiwatar da wasannin gargajiya na maza. Ana samun maroqa sosai suna aiwatar da sana'arsu ta roqo a fada gaban mai sarauta ko lokacin da yake zage ko rangadi. Makamancin haka kan faru a qofar gidan masu hannu da shuni ko masu riqe da wasu madafun iko a qasar Hausa.

**Sana'o'in Gargajiya Masu Alaqa da Roqo**

A wannan za a fito da jerin sunayen wasu sana'o'in gargajiya da suke da alaqa ta qut-da-qut da sana'ar roqo. Irin waxannan sana'o'i na qara armashi a wasu lokuta, in ana aiwatar da su tare da maroqa. Sana'o'in sun haxa da wanzanci, waqar baka da kixe-kixe da kuma wasannin maza na jarunta, kamar wasan dambe da kokowa (Hira da Tunkiya Ingawa).

**Kixi da Waqa**

Sana'ar kixi da waqa sana'o'i ne da maroqa suke da alaqa makusanciya da su. Duk yawanci in da ake aiwatar da waxannan sana'o'i za ka samu maroqa a wurin. Bayan haka, maroqa na taka muhimmiyar rawa sosai a cikin waxannan sana'o'i (Tsoho: 2010 da Idi Mai Kalangu). Wata muhimmiyar dangantaka da ke tsakanin maroqa da kuma makaxa da mawaqa ita ce ta asali. A yanzu akwai maroqa da yawa da, asali makaxa ne, wato sana'ar kixi suke a da, yanzu kuma sun koma roqo (hira da Abu Ingawa da Musa Na Akata Sanqiran `Yanxakan Katsina, Hakimin Dutsinma). Misalan irin waxannan makaxa da ke jihar Katsina da suka bar kixi suka koma sana'ar roqo sun haxa da Idi Mai Kalangu Kurfi da Alhaji Xan Kirki da Ummaru Dunvulai da Akilu Barde Na Namata da (hira da Idi Mai Kalangu Kurfi) da Sule Wanzan Gidan Bango Kusada da Lawal Sanqiran Hakimin Dutsinma (hira da Abu Ingawa) da kuma Sale Mai Rawa Qoroso (hira da shi a masallaci dtm).

**Wanzanci**

Wanzamai abokan tafiyar maroqa ne. kamar xan wa da xan qane suke a wajen sana'a (hira da Tunkiya Ingawa da Abubakar Wali Ingawa Ingawa). Da yake wanzamai bas a yanke kuxin ko ladar aikinsu, suna haquri da duk abin da wanda suka yi wa aiki y aba su, sun haqqaqe cewa, sun fi samun kuxi/lada mai tsoka a yayin da suka aiwatar da wasu daga cikin ayyukansu tare da maroqa. Misalign irin waxannan ayyuka na maroqa sun haxa da katciya/shayi da kuma yi wa jariri aski (hira da Tunkiya Ingawa). Irin wannan alaqa in ji Tunkiya Ingawa ce ke haddasa sa wasu wanzamai kama sana'ar roqo. Abin nufi a nan shi ne, wasu wanzaman kan kama sana'ar roqo saboda muhimmancin roqon a cikin sana'arsu ta wanzanci. Misali a yayin da wanzami ya je wajen yi wa yara kaciya ba tare da maroqi ba, in yana tare da

wani yaro kokuma shi kanshi, na iya miqewa ya shelanta a kawao kari. Da haka da haka, sai bakinsa ya buxe ya kama sana’ar roqo gadangadan (Tunkiya). Misalan maroqan da a da wanzamai ne a jihar Katsina sun haxa da Tunkiya Ingawa da Sule Wanzan Kusada ( Hira da Sule Wanzan Gidan Bango Kusada da Tunkiya Ingawa)

**Wasannin maza manya**

Kasancewar roqo na da muhimmanci wajen tunzurawa da kuma gwarzantawa, ya sa yake da muhimmancin qwarai ga masu sana`ar nuna qwazo na mazantaka. Irin waxannan sana`o`i bas u cika qayatarwa ba in babu maroqa. Misalan wassannin/sana`o`in gargajiya na maza masu buqatar maroqa sun haca da dambe da kokowa.

**Sarauta**

Hakimai da sarakuna na jihar Katsina na mu’amala sosai da maroqa. Hakan ne ya sa kowane hakimi ko sarki na da wani maroqinsa/maroqansa. Masu riqe da madafun iko na gargajiya sun kasance manyan iyayen gidan maroqa. Maroqa da dama sun ambaci hakimai da sarakuna a matsayin manyan iyayen gidajensu. Misali ‘Yan Dakan Katsina, Hakimin Dutsin-ma na da maroqinsa Musa Na Akata Sanqira, Maraxin Katsina, Hakimin Kurfi na da Abdulkarim Rabo a matsayin maroqinsa, Hakimin Ingawa na da Ma`abba Abdullahi Xan Ma`abba Sarkin Bambaxawa da Sarkin Roqo Alhaji Wali a matsayin maroqansa. Abin kuma bai tsaya nan ba domin dukan sauran hakiman na da nasu maroqan.

**Sana’ar Roqo A Yau: Havaka Ko Raunana**

Gaskiya sana`ar roqo a wannan zamani tana samun naqasu ta fuskoki da dama. Babbar fuskar da ta bayyanar da raunanar roqo a qasar Hausa ita ce ta yawan maroqa. Qimar roqo a sukar mutane ma ta qara tavarvarewa. Hakan na sa wasu `ya`yan maroqan bas a gadon iyayensu. Wannan lamari kuwa na rage yawan maroqa in an kwatanta da yawan waxanda ke shiga sana1ar ba tare da gadonta ba. Misali daga cikin Wali Sarkin Maeoqan Ingawa akwai wani da ya yi kuka da hawaye don an naxa maihaifin nasu Sarkin Roqo (hira da Abu Wali Ingawa)

**Tarihin Wasu Maroqa na Jihar Katsina**

**A) SANQIRA MUSA LAWAL NA AKATA TAKA TSABA**

MUSA LAWAL Na Akata Taka Tsaba shi ne Sanqiran `Yanxakan Katsina, Hakimin Dutsinma. Shi haifaffen garin Taka Tsaba ne kuma ya gaji sana`ar roqo da kuma miqaminsa na sanqira daga mahaifinsa mai suna Lawal Sanqira. An haife shi a wajen shekarar 1955. A yanzu ya kai shekara sittin da biyar ke nan. Kamar yadda wasu maroqa suke, kakan Musa Na Akata makixi amma kuma sai babansa ya koma ma roqo shi kuma ya gada daga baban nasa. Malam Musa ya koyi sana`ar roqo ga babansa. Ya riqa bin sa zuwa Katsina tare da uban gidansu `Yandakan Katsina, tun lokacin da ana tafiya a qasa har Katsinan.

Ya samu sarautar roqo, wato Sanqira bayan rasuwar mahaifinsa, Sanqira Lawal. Kuma, kamar ma fi yawan abokansa, bai samu dammar yin karatun book ba, amma dai ya yi karatun allo na addinin musulunci kaxan. NA Akata ba ya da wata sana`a sai ta roqo. A kan ta ya dogara wajen biyan buqatunsa. A maganar da ake yanzu yana da mata da `ya`ya da jikoki, sai dai kash bay a da magaji a sana`ar roqo. Har ya zuwa yanzu bai fidda ran samun magaji ba daga cikin `ya`yansa tun da suna da yawa ba. Ya ce karatun zamani ne ya sa yaran bas u xauka ba har yanzu.

Shi Musa bay a bin makaxa wajen aiwatar da sana`arsa. Amma fa in ta haxa su suna yi ayyukansu a tare kowa na cin gashin kansa. Ba a matsayin yaro da maigida ba. Yana yin roqonsa ga masu kuxi da masu riqe da madafun iko. Kuma yana aiwatar da aikinsa a wajen buki ko suna ko kuma kowane irin taro aka haxa. Babban uban gidansa dais hi ne `Yanxaka. Daga shi kuwa sai sarkunan noma kamar Lezumawa.

A sana`ar roqo yake aiwatar da komai na rayuwarsa. Yana samun kyautar kuxi da abinci da kuma suture. Duk shekar sai `Yanxaka ya yi masa xinki na asun da saun. Sarakunan noma na bas hi kuxi da abincin da za ya ci. Sanqira ta ce ba a tava bas hi kyautar abin haw aba. Amma an tava ba babansa doki. Kuma har yanzu dokin yana nan.

KIRARIN `Yanxaka Sada

`Yanxaka Sada
Sada Magajin Sada
Xan Mamman magajin Mamman

Mamman Gixaxo magajin Gixaxo
`yanxakan Katsina Hakimin Dutsinma
In ka taho kallo ya zo
In ka wuce kallo ya qare
Xan Sada jikan Mani
Allah ya jiqan `Yanxaka Zubairu
Allah ya jiqan Mani
Allah ya jiqan Abdu
Allah ya jiqan Bala uban Bala xan Sada
Allah jqan Magaji Muhammed
Allah jiqan Hajiya Iya,
Allah Jiqan Hajiya Hali

Ga kuma kirarin Lezumawa

Gansoqa na qoqi kibau
Waxanda ba ku daxin gaba
Tuwaru uwar magani
Zummuwa da daxi da faxa
Gamsheqa ko kin san mutum ki nai mai faifai
Aska ba ki amana ko kin ci mutum kina

**B ABUBAKAR WALI SARKIN ROQON DAMBO HAKIMIN INGAWA**

Shi Abubakar Wali xa ne ga Muhammadu Inuwa Wali, Sarjin Roqon Danbo Hakimin Ingawa. Hakan ya nuna gado ya yi kamar yadda mahaifinsa ma gadon sana`ar roqo ya yi daga mahaifinsa. Su dama `yan asalin kuma mazauna garin Ingawa ne. Abubakar Wali ba shi da wata sana`a a duniya da ta kai ta roqo. Kamar yadda ya bayyana mani, komai aka gani a gidansa, ya same shi ne ta sana`ar roqo. Da roqo ya yi aure da kuma roqon yake riqe da gidansa.

Dangane da ilimin zamani na book, Abubakar bai yi zurfi ba, domin karatunsa bai wuce na sakandare ba. Ilimin addini ma abin cikin cokali ne.

Mahaifin abubakar, wato Alhaji Wali ya mutu ya bar `ya`ya maza har tara kuma shi Abubakar xin shi ne qaramin cikin su. Kaf a cikinsu kuwa ba mai yin roqo sai shi abubakar xin. Shi kuma ya xauki ya yi wannan sana`a domin ya share ma mahaifinsa hawaye a dangane da ci gaba da samun wanzuwar sana`ar a cikin zuriyarsu (Hira da Abubakar Wali Ingawa). Haka kuma shi Abubakar xin ya gamsu da wannan sana`a ta roqo, don haka ne ma ya sha alwashin, dole in Allah ya yarda sai ya samu magaji a cikin zuriyarsa dangane da sana`ar roqon. Abubakar ya koyi sana`ar roqo daga mahaifinsa. Abubakar kan yi wa mahaifinsa kirari. Mahaifin nasa na kuma jin daxin wannan kirari da xansa ke masa. A yanzu ba ya da ubangida a sna`ar rook kamar Sarkin Banbaxawan Dambo. Babban ubangidansa da yake wa roqo kuwa shi ne Hakimin Ingawa.

Abubakar ya xauki huxubar babansa dangane da haquri da kula tare da adalci ga maroqa. Hakan ya say a ce ba ya da maqiyi a cikin sana`ar ta roqo. Yana samun goyon bayan `yan uwansa maroqa na yankin Ingawa kaf.

Shekarun Abubakar Wali a yanzu sun kai arba`in da uku (43) a duniya. Ton yana da shekara talati (30) a duniya ya fara sana'ar roqo kenan, a yanzu kuma ya yi shekaru har goma sha uku (13) a cikin wannan sana`a. A yanzu haka Abubakar Wali yana koya wa xiyarsa sana'ar (yana tura ta sanarwar allurar foloyo). Saboda sha`Wr sana`ar roqon da yake matarsa ma xiyar maroqa ce. Hakan ya sa ba ya shakkun samun magaji a cikin zuriyarsa.

Ga wani daga cikin kirarin da yakan yi wa Dambo Hakimin Ingawa:

Allah ya jiqan Dambo Abubakar
Allah ya jiqan Balaraben sarki
Dambo Sulaimanu, Allah shi gafarta mashi

Tukur magajin Tukur.
Allah jiqan Dambo Ibrahim
Allah jiqan Dambo Iro
Allah jiqan Dambo Abubakar

**C) IDI MAI KALANGU KURFI**

Idi mai kalangu mazaunin garin Kurfi a Qofar Arewa ne. Sunan mahaifinsa Barau Makaxi. Duk da kasancewar malam Iyak an tava wasu `yan sana`o`i kamar su kiwon qananan dabbobi da sayar da kara ga masu buqatar toyawa ko wani abu da igiya da ganyen dabbobi, ba ya da wata sana’ar da ta fi ta roqo a rayuwarsa. Amma fa abin da ya gada kaka da kakanni a gidansu shi ne sana`ar kixi. Da shi da Sani da Halliru qannensa duk sun iya yin kixi, amma fa a yanzu in ban da Halliru kaxai, duk sun bar yin kixi sun koma sana`ar roqo. Shekarun Idi Mai Kalangu Kurfi a yanzu sun kai shekara saba`in da shida (76).

Cikin `ya`yan Idi Mai Kalangu ba wanda ya gaje shi wajen sana`ar roqo ko kixa. An tava neman a naxa shi sarkin maroqa amma ya qi. Ya yi hakan ne ba domin qyamar sana`ar ta roqo ba, illa kaxai saboda shi kixa ya gada a gidansu. Saboda haka, yana ganin koma baya ne ya kama sarautar roqo.

Yana roqo a wurin taro ko wane iri. Bai koya wa yaransa sanar roqo ko kixa ba saboda yana ganin zamani na addini da ilimi yana sukar hakan. Wannan na nuna cewa a halin yanzu Idi Mai Kalangu ba shi da magajinsa daga cikin `ya`yansa.

Manyan kyautukan da ya samu, sun haxa kyautar da Xan Arewa da Xayyabu Dagatta ta dubu ishiri-ishirin a 2018 da 2019.

Misalin roqonsa

Alhaji Ibrahim Maidabino
Allah taimake ka da taimakonsa
Allah ya qara farin jini da xaukaka
Allah ya kare gabanka da bayanka
Ina fatar Allah ya taimake ka Malam Ibrahim

**Sunayen Wasu Maroqa a Jihar Katsina**

| NA | SUNA | GARI | GADO? |
|---|---|---|---|
| 1 | Murtala Magaji | Babban Mutum | E |
| 2 | Sale `Yarmagyafa | Babban Mutum | E |
| 3 | Sani Ramamme | Babban Mutum | E |
| 4 | Dauda Isa | Babban Mutum | E |
| 5 | Bala Mashi | Dageji | E |
| 6 | Audu Tsoho Tama | Tama | E |
| 7 | Baban Bello | Tama | A’a |
| 8 | Ummaru Gaya | Gaya | A’a |
| 9 | Malam Mati | Zangon Tama | A’a |
| 10 | Idi Na Girexo | Zangon Tama | E |
| 11 | Da’u Dageji | Dageji | A’a |
| 12 | Xan Kwabo Dageji | Dageji | A’a |
| 13 | Amadi Xan Kora Javo | Javo | A’a |
| 14 | Sari Dosa | Rigar Suri | A’a |
| 15 | Namaredu Giwa | Katakulu | A’a |
| 16 | Kwalabe Jabo | Kusada | A’a |

| | | | |
|---|---|---|---|
| 17 | Shehu `Yar Qafa | Dageji | A’a |
| 18 | Mu’azu Muda | Gaiwa | A’a |
| 19 | Sare | Kusada | E |
| 20 | Audu Mai Buta | Gaiwa | A’a |
| 21 | Barin Gari | Hayin Gaiwa | A’a |
| 22 | Xan Tiri Kwamri | Kamri | E |
| 23 | Tanimu Jikan Makaxa | Bindawa | E |
| 24 | Ule Dallaji | Dallaji | E |
| 25 | Sarkin Mamarawa | Dallaji | E |
| 26 | Amuta Dallaji | Dallaji | E |
| 27 | Na’ayyi Dageji | Dageji | E |
| 28 | Mummuni Dageji | Dageji | E |
| 29 | Xan Mage | Dageji | E |
| 30 | Lalu dageji | Dageji | E |
| 31 | Na Lado Dageji | Dageji | E |
| 32 | Hashimu Rigar Vuri | Rigar Vuri | E |
| 33 | Iliya Kan Dave | Bindawa | E |
| 34 | Ramu Mai Kixan Qwarya | Bindawa | A’a |
| 35 | Maikuxi Magaji Hassan (F) | Bindawa | A’a |
| 36 | Uwar Biyu Mai Kumbo | Bindawa | A’a |
| 37 | Yalo Tama (F) | Bindawa | A’a |
| 38 | Alhaji Abdurrashid | Rinjin Baushi (S/Maroqa | E |
| 39 | Musa Kakaki | Xandume | E |
| 40 | Audu Gemu | Xandume | E |
| 41 | Mu’azu Mai Kalangu | Xandume | E |
| 42 | Musa Sakataren Maroqa | Bindawa | E |
| 43 | Aminu Mu’azu Mai Kalangu | Bindawa | E |
| 44 | Sokana Jiruwa | Bindawa | E |
| 45 | Xanlami Roki | Mahuta | E |
| 46 | Magaji mai kalangu | Mahuta | E |
| 47 | San Qira Iro | Mahuta | E |
| 48 | Aliyu Nakwayya | Kanga | E |
| 49 | Namakaxa | Xanmusa | E |
| 50 | Sakatare Maroqi | Riga Tashar Icce | E |
| 51 | Ibrahim Nagoxi | Xanmusa | E |
| 52 | Bello Nawake | Maidabino | E |
| 53 | Alhaji Sani Cinbisko | Xanmusa | E |
| 54 | Boqon Baqi | Xantudu | E |
| 55 | Xan Alhaji Bagobiri | Kanga | A’a |
| 5556 | Ibrahim Sanqira | Xanmusa | E |
| 57 | Uman Qodago | `Yantumaki | E |
| 58 | Ibrahim Garba | Xanmusa | E |
| 59 | Kasahi Tashar Qaura | Tashar Qaura | E |
| 60 | Rabe Wakili | Xanmusa | E |
| 61 | Hamisu mai Bindiga | Xanmusa | E |
| 62 | Bala Xankazagi | Xanmusa | E |
| 63 | Ummaru Sanqira | Xanmusa | E |

| | | | |
|---|---|---|---|
| 64 | Rabe Uwar Kare | Xanmusa | E |
| 65 | Haruna Nasarawa | Nasarawa | E |
| 66 | Namadawa Xantakuri | Xantakuri | E |
| 67 | Abdullahi Xan’ali | Xan’ali | E |
| 68 | Mamuda Sulemana | Xanmusa | E |
| 69 | Bala Old Gurza Gg | Gurza | E |
| 70 | Rugar Nabage | Xanmusa | E |
| 71 | Bello Falale | Falale | E |
| 72 | Ashiru Na Gindin Kanya | Gindin Kanya | E |
| 73 | Alhaji Xan Kirki | Xarawa | E |
| 74 | Iliya JIkan Bukku | Karofi | E |
| 75 | Malam Haruna Faru | Qadangaru | E |
| 76 | Malam Iliya Qarago | Dutsinma | E |
| 77 | Ummaru Dumvulai | Qadangaru | E |
| 78 | Alhaji Usman Shagali | Qadangaru | E |
| 89 | Abdullahi Saga | Qadangaru | E |
| 80 | Malama Rahinat Lahi | Dutsinma | E |
| 81 | Iliya Birde Hayin Qorama | Karofi | E |
| 82 | Yakubu  Tanki | U/Tsamiya Kwantamawa | Gado |
| 83 | Nababa S/Roqon Yanxaka | Kureci | Gado |
| 84 | Lado Jikan Kwaxo | Kwantamawa | Gado |
| 85 | Ale Dabawa | Dabawa | Gado |
| 86 | Musa Na Akata Sanqira | Taka Tsaba | Gado |
| 87 | Ibrahim Nalungu | Taka Tsaba | Gado |
| 88 | Sa’idu Wali | Dutsinma | Gado |
| 89 | Kabir Malam | Dutsinma | Gado |
| 90 | Sama Musa | Dutsinma | Gado |
| 91 | Mu’azu Cido | Dutsinma | Gado |
| 92 | Malam Bala Cido | Dutsinma | Gado |
| 93 | Bala Sanqira Musa | Dutsinma | Gado |
| 94 | Dikko Kabir | Dutsinma | Gado |
| 95 | Zakawanu Sama’ila | Dutsinma | Gado |
| 96 | Alasan Bala | Dutsinma | Gado |
| 97 | Sale Mai Rawa Qoroso | Dutsinma | A’a |
| 98 | Alhaji Isa Jijji | Dutsinma | Gado |
| 99 | Shu’aibu Tambai | Dutsinma | Gado |
| 100 | Malam Ado | Dutsinma | Gado |
| 101 | Manin Gamba | Dutsinma | Gado |
| 102 | Ayuba Walaru | Walaru | Gado |
| 103 | Alhaji Shagali | Qadangaru | Gado |
| 104 | Aqilu Barde Na Namata | Dutsin-ma | Gado |
| 105 | Buji Ibrahim | Dutsinma | Gado |
| 106 | Lawal Sada | Dutsinma | Gado |
| 107 | Lawal Kwatahi | Dutsinma | A’a |
| 108 | Nababa Jikan Toka | Dutsinma | Gado |
| 109 | Abdulhamid Shawai | Dutsinma | Gado |
| 110 | Sani Arje | Dutsinma | Gado |
| 111 | Sule Kobarawa | Dutsinma | Gado |
| 112 | Sada Dagelawal | Dagelawal | Gado |

| | | | |
|---|---|---|---|
| 113 | Na'andi Sabar | Sabaru | Gado |
| 114 | Ibrahim Bagobiri | Ashata | Gado |
| 115 | Bala Na Alti Dogon Qarfe | Dutsinma | A'a |
| 116 | Auta Xanmalam | Dutsinma | A'a |
| 117 | Damen Qaya (Barinje) | Ruwan Xorawa | A'a |
| 118 | Mai Hilani Ruwan Xorawa | Ruwan Xorawa | Gado |
| 119 | Rabe Ruwan Xorowa (Makadi) | Ruwan Xorowa | A'a |
| 120 | Lawal Ruwan Xorowa | Ruwan Xorowa | Gado |
| 121 | Hassan Liba | Shantalawa | Gado |
| 122 | Gambo Qyadi | Shantalawa | Gado |
| 123 | Lawal Mati Shantalawa | Shantalawa | Gado |
| 124 | Audu Sha'ani | Shantalawa | Gado |
| 125 | Sale Wakaji | Wakaji | Gado |
| 126 | Gambo Makaxi 'Yanruma | 'Yanruma | A'a |
| 127 | Wanga Turare | Turare | A'a |
| 128 | Garba Turare Bagobiri | Gidan Kamvai | Gado |
| 129 | Tukur Shagali | Dutsinma | Gado |
| 130 | Xahiru Xantuttu | Dutsinma | A'a |
| 131 | Ado Nadede Maikixi | Dutsinma | A'a |
| 132 | Ilu Diddige | Kwari Maizurfi | Gado |
| 133 | Ado Ciki | Vagagadi | Gado |
| 134 | Abu Vulle | Vagagadi | Gago |
| 135 | Sa'idu Bala | Vagagadi | A'a |
| 136 | Shehu Adamu Mai Kifi | u/mai Kanwa Faskari | A'a |
| 137 | Inuwa Xan Abu | Faskari | Gado |
| 138 | Muhammad Inuwa Xan Abu | Faskari | Gado |
| 139 | Usman Tambai | U/Barau Faskari | Gado |
| 140 | Hashimu Adamu | Faskari | Gado |
| 141 | Yusuf Mai Dala'ilun Roqo | Faskari | Gado |
| 142 | Lawal Magin Roqo | Faskari | Gado |
| 143 | Ado mai Biri | Faskari | Gado |
| 144 | Hassan Canji | Faskari | Gado |
| 145 | Sani Marafa Makaxi | Faskari | Gado |
| 146 | Bishir Wanke-wanke mai Gurmi | Faskari | Gado |
| 147 | Lawal Okoca Mafarauci | Faskari | Gado |
| 148 | Bello 'yar Murya | Ingawa | Gado |
| 149 | Sani Haske Yandoma | Yndoma | Gado |
| 150 | Alhaji Abu Dogo | Yandoma | Gado |
| 151 | Sale Tumburi | Yandoma | Gado |
| 152 | Abdullahi Ma'abba | Bambaxawa | Gado |
| 153 | Idi Yaro | Kaita | Gado |
| 154 | Sani Haske Yandoma | Yndoma | Gado |
| 155 | Alhaji Abu Dogo | Yandoma | Gado |
| 156 | Sale Tumburi | Yandoma | Gado |
| 157 | Zulai Wakaji kyaras | Kankiya | Gado |
| 158 | Safiya Bara`u | Sabuwar Mara | Gado |
| 159 | Ummaru Da`ayi | Kankiya | Gado |

| | | | |
|---|---|---|---|
| 160 | Ummaru Mare-mare | Kafin Soli | Gado |
| 161 | Yahaya San Qira | Kafin Soli | Gado |
| 162 | Idi Yaro Wazirin Roqon S/Sulluvawan Kt | Katsina | Gado |
| 163 | Ibrahim Mara Mara | Kambarawa Kt | Gado |
| 164 | Ushe Maroqi | Katsina Tudun Wada | Gado |
| 165 | Salmanu Maroqi | Katsina Qerau | Gado |
| 166 | Daxi Maroqi | Katsina Lalloki | A’a |
| 167 | Sule Maroqi | Katsina ‘Yan Shanu | Gado |
| 168 | Dauda Xan Shila | Katsina Gafai | A’a |
| 169 | Sani Lauje | Katsina’Yan Qaure | Gado |
| 170 | Sabe Zarto | Katsina Yammawa | Gado |
| 171 | Usman Kazagi | Katsina Rafukka | Gado |
| 172 | Dashe Maroqi | Katsina Katsire | A’a |
| 173 | Shamsu Bula | Katsina K/Marusa | Gado |
| 174 | Sambo Xan Kunama | Katsina Rafin Daxi | Gado |
| 175 | Shatu Maroqiya | Katsina Saulawa | Gado |
| 176 | Karima Reza | Katsina Galadanci | Gado |
| 177 | Zaliha Maroqiya | Katsina Gwangwan | A’A |
| 178 | HARO | Qauyen Laya | Gado |
| 179 | Babangida (Ummaru) | Qauyen Laya/Gundoji | Gado |
| 180 | Babangida (Abba Mai Gadaje) | Samro Tinya | A’a |
| 181 | Isa Rika | Tsauri | Gado |
| 182 | Isa Mariqi | Kusada | Gado |
| 183 | Mani Mairoqo | Kusada | Gado |
| 184 | Sa’adu Usman | Dudunni | A’a |
| 185 | Abubakar Garba | Isawa | Gado |
| 186 | Sule Wanzan | Gidan Bango | Gado |
| 187 | Idris Gwamna | Xangamau | Gado |
| 188 | Sale Mai Qusa Tuttuqe | Tuttuqe Xangamau | Gado |
| 189 | Yahaya Gana | S/ Garin Xangamau | Gado |
| 190 | Bello mai Qorai | Shemar Xangamau | Gado |
| 191 | Bado Keva | Keva Xangamau | A’a |
| 192 | Camama Unguwar Quli | U/Quli Xangamau | A’a |
| 193 | Bello Na Gwandu | Kuka Huxu | Gado |
| 194 | Audu Xan Shibo | Kwalliya | A’a |
| 195 | Idi Sarkin Aiki | Gidan Sarkin Aiki | A’a |
| 196 | Mati Na Gyandu Kuka Huxu | ‘Yartsamiyar Jino | Gado |
| 197 | Ibrahim na Gyande | Tsamiyar Jino | Gado |
| 198 | Gambo Gurgu | Xan Marke | Gado |
| 199 | Sani mai yaji | Majifa | Gado |
| 200 | Bature Ango | Qanqara | Gado |
| 201 | Liti Na Qawari | Xanmurabu | Gado |
| 202 | Sani Caxuwa | Fawwa | Gado |
| 203 | Bala Eriya | Unguwar Na Goxi | Gado |

| | | | |
|---|---|---|---|
| 204 | Garba Kwaram | Majifa | Gado |
| 205 | Jamilu mato (Na Gagu) | Vaure | Gado |
| 206 | Binta Ragaya | Burdugau | Gado |
| 207 | Abdullahi Kilin Maroqi | Tuge | Gado |
| 208 | Musa Gishirin Biki | Tuge | Gado |
| 209 | Ado Maroqi | Tuge | Gado |
| 210 | Garba Girado | Tuge | Gado |
| 211 | Usman Hambali | Tuge | Gado |
| 212 | Garba Gayya Maroqi | Tuge | Gado |
| 213 | Hassan Xan Talau | Tsohuwar Kasuwa | Gado |
| 214 | Malam Talau | Tsohuwar Kasuwa | Gado |
| 215 | Sanusi Alheri | Malunfashi | Gado |
| 216 | Xanyar Hura | Fayamasa MLF | Gado |
| 217 | Abubakar Muhamman | Bayan Kasuwa | Gado |
| 218 | Abdulkarim Xan Tsoho | `Yar kwakware Mlf | Gado |
| 219 | Ya’u Guma | `Yar kwakware Mlf | Gado |
| 220 | Malam Usman Kwanar Wari | Hayin Majima Mlf | Gado |
| 221 | Isiyaku Maroqi Layin Shanu | Malumfashi | Gado |
| 222 | ‘Yar Akuya | Tsohon Dam Mlf | Gado |
| 223 | Alh Ado Mani Sanqiran Durvi | Mani | Gado |
| 224 | Vula Vula Xab Kantoma | Bagiwa | Gado |
| 225 | Abdu Xanye-Xanye | Bagiwa | Gado |
| 226 | Na Tanyo Mani | Mani | Gado |
| 227 | Xan Kurkutu Jani | Jani | Gado |
| 228 | Kanawa Jani | Jani | Gado |
| 229 | Sama;ila Na Yawale | Muduru | Gado |
| 230 | Mati Ibrahim Man Gyaxa | Muduru | Gado |
| 231 | Bawale Yaro | Muduru | Gado |
| 232 | Haruna Haro Mai Kaka | Muduru | Gado |
| 233 | Musa Kangoli | Karfawa Muduru | Gado |
| 234 | Maikuxi Mai Qarfi | Riya Muduru | Gado |
| 235 | Amadu Na Babi Gwajo | Gwarjo | Gado |
| 236 | Namakaxa | Gwarjo | Gado |
| 237 | Ibrahim Kuido Na Babi | Runka | A’a |
| 238 | Ado Gemu | Runka | A’a |
| 249 | Audu Saro sanqira | Xandume | Gado |
| 240 | Ummaru Amadu Sanqira | Xandume | Gado |
| 241 | Amina mu’azu | Xandume | Gado |
| 242 | Ado Sakatare | Xandume | Gado |
| 243 | Adamu Valla Baka | | Gado |
| 244 | Habu Xanlami | Mahuta | Gado |
| 245 | Ummaru Xandamo | | Gado |
| 246 | Abubakar Ana Ruwa | | Gado |
| 247 | Muhammadu Haji Auta | | Gado |

| | | | |
|---|---|---|---|
| 248 | Rabi'u Tsan | | Gado |
| 249 | Yakubu Xanwake | Gugar Mahuta | Gado |
| 250 | Sani sani siloana | Xayau Xandume | Gado |
| 251 | Zanko 'Yardaje | Kuli 'Yardaje | Gado |
| 252 | Alh Mamman Takoci | Kwarin Kuxe 'Yardaje | Gado |
| 253 | Xandisko i Kwanda2 | 'Yardaje | Gado |

**Qiyasin Adadin Maroqa A Jihar Katsina**
**Sakamakon Bincike**
Abin da wannan bincike ya gano ya haxa yawan maroqan dake jihar Katsina da qiyasinsu ya kai mutum dubu huxu. Binciken ya bayyana cewar masu wasu sana'o'in kamar kixi da wanzanci kan rikixa su koma maroqa saboda kyajjyawar dangantakar masu sana'ar.
**Pie Charts 1. Magada da maroqa 2 by lga 3 by sex, 4**
**Kammalawa**

**ACKNOWLEGEMENT**
This work was supported by Isa Kaita College of Education Dutsin-ma, Katsina State, throught the TETFund intervention program on Institution Based Research (IBR) grant number TETF/DR & D/CE/CEO/KATSINA/IBR/2024/VOLIII.

**Manazarta**
Facts on File (2005) The Encyclopedia of Novel into Film (Facts on File Film Reference Library). Ana saukarwa a http://hotfile.com /dl/57884912/6eb1056/0816054495.pdf.html ko a http://www. fileserv.com/file/rp8q2RQ
Furniss. G. (1996) *Poetry, Prose and Popular Culture in Hausa*. Edinburgh: Edinburgh University press.
Gusau. S. M. (2005) *Makaxa da Mawaqan Hausa*. Kano: Benchmark Publishers Limited.
Gusau. S. M. (2008) *Waqoqin Baka a Qasar Hausa*. Kano: Benchmark Publishers Limited.
Tsoho, M. Y. (2010). Sanqira: Gudunmuwarsa a Gina waqoqin Yabo. Muqalar da ya gabatar a cikin Mujallar *Harshe Journal of African Languages 4*. Zaria. A. B. U.

WAXANDA AKA YI HIRA DA SU
Abdullahi Ma`abba Sarkin Bambaxawan Dambo
Abu Wali Satkin Roqo Ingawa
Haro Maroqi qauyen Laya ranar
Idi Mai Kalangu Kurfi
Musa Na Akata Lawal Sanqiran Yandakan Katsina Hakimin Dutsin-ma
Sule Wanzan Gidan Bango Kusada
Tunkiya Ingawa ranar